




Amina mai Gaskiya
Littafin karatu a sauƙaƙe - Mataki na 4
Hausa

Zuwa ga malamai da iyaye:

Kafin a fara amfani da wannan tsarin koyon karatu, dole sai ɗalibi ya: • San amon sautukan haruffan Hausa; • Iya gane kalmomin da aka saba da su.

Amina mai Gaskiya
Hausa Nigeria

Copyright © 2017, Enabling Writers Project - American University of Nigeria


http://creativecommons.org/licenses/by/4.0/
http://creativecommons.org/licenses/by/4.0/ An yarda ka yi amfani da wannan aikin ta wajen harkar kasuwanci. Kana iya ɗaukar aikin nan a yadda ya ke ko ka yi ƙari akai. Dole ne ka ajiye hakkin mallaka da kuma alaƙanta aiki ga marubuta, masu zayyana da sauran su. ISBN

Grace Malgwi Writing Trainer/Collection Editor
Prof Salisu Yakasai and Prof Lawan D Yalwa Hausa Language Consultants
Nas Yakubu Bloom Trainer
Story Writers Husaini Adamu; Adamu Babbikoi; Garba Mohammed Dantsoho; Jalauddeen Ibrahim Maradun; Yasalu Haruna; Muhammed Umar Deba; Idris Hamid; Ibrahim Baraya; Dahiru A Yelwa; Mansur Isah Buhari; Grace Malgwi
Illustration from International Illustration:The Art of Reading 3.0 Copyright:  SIL International 2009





Amina yarinyar kirki ce.
Tana da ladabi a gun kowa.
Amina ba ta ƙarya ko kaɗan.
Kirkinta ya sa babanta ya na son ta.
Kirkinta ya sa innarta ta na son ta.
Kirkinta ya sa kowa ya na son ta.



Amina na a kan hanyar zuwa makaranta.
Sai ta yi tsintuwar fensiri.
Ta san ba nata ba ne.
Don haka ba ta saka a jakarta ba.
Ta riƙe fensirin a hannunta.
Ta nuna wanda ya yar ya gani.

Har Amina ta isa makaranta ba mai fensiri.
Amina ta kai wa shugaban makaranta fensirin.
Shugaban makaranta ya tambaye ta ina ta samu.
Amina ta ce kan hanyarta zuwa makaranta.
Shugaban makaranta ya karɓi fensirin.






Yara sun dawo daga cin tara.
Malam ya shigo ajinsu Amina.
Malam ya ba su gwaji.
Kowane yaro ya na rubutu.
Yaro ɗaya ba ya rubutu.
Malam ya tambaye shi dalili.
Ya ce ya ɓatar da fensirinsa a hanya.

Malam ya ce ya tashi ya bar ajin.
Ba zai rubuta gwajin ba.
Yaron ya fara kuka.
Amina ta ji abin da ke faruwa.
Ta ce ta yi tsintuwar fensiri a hanya.
A ka je wurin shugaban makaranta.





Shugaban makaranta ya fitar da fensiri.
Fensirin na yaron ne.
Yaro ya gode wa Amina.
Malam ya gode wa Amina.
Shugaban makaranta ya gode wa Amina.
Amina ta zama shugabar ɗalibai don gaskiyarta.

ALL CHILDREN READING: A GRAND CHALLENGE FOR DEVELOPMENT

USAID FROM THE AMERICAN PEOPLE

World Vision

Australian Aid

GLOBAL READING NETWORK